# "Wanda ya manta alhali yana azumi, sai ya ci ko ya sha, to ya cike aziminsa, kaɗai Allah ne Ya ciyar da shi kuma Ya shayar da shi".

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi - ya ce: "Wanda ya manta alhali yana azumi, sai ya ci ko ya sha, to ya cike aziminsa, kaɗai Allah ne Ya ciyar da shi kuma Ya shayar da shi".
[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya bayyana cewa wanda ya ci ko ya sha akan mantuwa alhali shi yana cikin azimin farilla ko nafila to ya cika aziminsa kada ya karya; domin cewa shi bai yi nufin karyawa ba, kawai shi wani arziƙi ne Allah Ya koro masa kuma Ya ciyar da shi Ya shayar da shi.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee